# TARIHIN GANA-GANA DA AL'ADUN - SU

NA

HAJARA HALIDU
NO 3540-96

SASHEN HAUSA/PES
KWALEGIN ILIMI TA MINNA

NOVEMBER, 2000

LANG. 63

# *TARIHIN GANA-GANA DA AL'ADUN – SU*

*NA*

*HAJARA HALIDU*

*NO 3540/96*

*SASHEN HAUSA/PES*
*KWALEGIN ILIMI TA*
*MINNA*

SERIAL/DOCUMENTATION UNIT
LIBRARY DEPT.
C.O.E. MINNA

*NOVEMBER 2000.*

# TA KARDAR AMINCEWA

Na Gabatar da wannan aikinnawa domin amincewar mallama ta.

| | |
|---|---|
| ................................ | ................................ |
| **SA HANNUN DALIBA** | **SA HANNUN MAI DUBA WA** |
| 10/5/2001 | 10/4/2001 |
| ................................ | ................................ |
| **KWANAR WATA** | **KWANAR WATA** |

**SHIMFIDA:- TARIHIN GANA – GANA DA AL'ADUN SU**


**GABATARWA** iv

**CHAPTER ONE**

TRIHIN GANA – GANA DA KASARSU 1 – 3

**CHAPTER TWO: 1**

AL'ADAR AUREN GANA – GANA 4 – 7

1:2

IRE – IREN AUREN GANA – GANA.

AUREN SOYAYYA 5

AUREN TILAS

AUREN ZUMUNTA

**CHAPTER THREE** 8 – 11

HAIHUWA

**CHAPTER FOUR**

SUNA 12 – 13

IV: 1:- ZANA SUNA

IV: 2 WASAN SUNA

**CHAPTER V** 14

MUTUWA

**CHAPTER VI**

BUKUKUWA DAWASSANNI 15 – 16

Vi: 1 Bukin Sallah

Vi: 2 Bukin Suna

Vi: 3 Bukin Aure

Vi: 4 Bukin SABON DOYA

**CHAPTER VII**

DANGANTAKAR AL'ADUN GANA – GANA 17

DA

NA HAUSAWA.

## GABATARWA:-

Wannan dan littafin ya kunshi bayani ne akan tarihim Gana – Gana da al'adum su. Da farko anyi bayani kan al'alader auren su, da ire – iren aure, da kuma sai suna ire-ire sunayen gargajiya kuma wankar buki da goyo. Haka kuma da yadda ake sha'anin mutuwa da kuma yadda ake bukukuwa da wasannin su. Daga karshe zamu ga ire wasanni da ake yi na gargajiya. Sauran kuma sai Dangatakar da ke tsakanin al'adun Hausawa da na Gana – Gana.

## GABATARWA:-

Wannan dan littafin ya kunshi bayani ne akan tarihim Gana – Gana da al'adum su. Da farko anyi bayani kan al'alader auren su, da ire – iren aure, da kuma sai suna ire-ire sunayen gargajiya kuma wankar buki da goyo. Haka kuma da yadda ake sha'anin mutuwa da kuma yadda ake bukukuwa da wasannin su. Daga karshe zamu ga ire wasanni da ake yi na gargajiya. Sauran kuma sai Dangatakar da ke tsakanin al'adun Hausawa da na Gana – Gana.

# GODIYA

Godiya ya tabbata ga Allah madaukakin Sarki da Shugabanmu Annabi Muhammadu (S.A.W). Ina mika godiya ta ga mahaifina Alhaji Abubakar Jiwo Dangara Wanda ya rigamu gidan gaskiya Ubangiji Allah ya jikan sa domin na fara wannan kos ya na nan. Kuma ga shi yau zan gama ba shi nan ya riga mu gidan gaskiya Allah ya Gafarta msasa (Amin) shi ne ya sha wahalar ya sa ni a firamari da sakandare na gama ya kuma bani karfin gwiwa. Godiya ta ga mahaifiya ta Hajiya Nana Aishatu wadda ta haife ni ta kuma rene ni her ta zaunar da ni ta bani tarihin Gana-Gana da al'adunsu, Allah ya saka Mata da Alheri (Amin) ina mika godiya ta ga maigida na Alhaji. Haludu Adamu maishanu domin nauyin makaranta na da yayi na taimaka ma ni wajen biyan kudin makaranta daga farko her karshe Allah ya saka masa da Alheri. (Amin). A karshe na gode wa Hajiya Salamatu Jibiril Wadda ta duba mai aiki na ta kuma ba ni karfin gwiwa na kammala wannan. Aiki na wa it a ma Allah ya Saka mata da Alheriasa. Sauran malamai na wadan da su ka karantar da ni su ka bani nasu illmin musanman Malam Sule Ladan da Malam Aliyu M. Busa, Da malama Zainab, da Malam Aliyu I Fulani, da Malam Musa Sani Ahammed da sauran Malamai Allah ya saka masu da Alhreri

## DOMIN

Na rubuta wannan littafi domin mahaifi na da mahaifiyata, da ya'yana, Umar, Hassan, Hussaina, Maimuna da Adamu da kuma malamai na wadanda suka koyar dani Allah ya saka musu da Alheri ( Amin).

SERIAL/DOCUMENTATION UNIT
LIBRARY DEPT.
C.O.E. MINNA

# CHAPTER I

## CHIMFADA:

## TARIHIN GANA-GANA DA KASAR SU

A salin Gana-gana dai Nufawa ne saboda shi tsode wanda yake shi ne asalin Nufawa yana da kani wanda a ke kiransa Muhamamadu Gana-ko shi wannan Muhammadu Gana-ko yayi hijira saboda yake-yake da akayi domin shi wansa tsode ya umurce shi da zuwa gaba saboda ya yake sauran garuruwa. Daga nan shi Muhammandu Gana-ko ya tashi zuwa Gbara ga Gbara zuwa Nupeko, daga nan sai ya sauka a Agaie, to da Nufawa suka same shi sai suna kiran shi Etsu-Agaieci saboda sun same shi ne a wurin. Ma'anar wannan suna. Kuwa ita ce sarkin Agaie to da yaga yana da niyar zuwa gaba, sai ya bar Agaie zuwa kasar Gulu in da ya kafa bukkar sa. Su kuma Nufawa. Suka maimaye. Agaiede da kewayensa.

Shi Muhammadu ya cigaba da zaman sa a Gulu har ya same mata ya Aura wadda ake kira A wushetu watau Aishatu. Allah ya basu haihuwa, yayan-su hud'u, uku maza mace daya. Yana zaune da matarsa suna sana'ar, kama kifi har 'ya'yan nan sun girma sai ya sa. Su zuwafataueci kasar Gara, har daga nan su ma suka samu wajen zuwa har su ka yada iri wanda yau kasan Gara ya yad'u.

Shi wannan Muhammadu Gana-ko, kamar yadda na fadi da farko sana'ar sa kamar kifi ne to yana cikin wannan sana'ar ke nàn, shi bai iya hawan gora ba domin yana kama kofi da kurgiyane sai Hausa wa masunta suka zo suka sauka a gidan sa suka koya masa yadda ake hawan Gora a kama kifi da kuma anfani da kalli domin samun kifaye da yawa. Haka ya saba da wadanan Hausawa suma sun saba da shi har suka zama abokain Juna kowane shekara gidan sa suke sauka saboda sabo.

To wadannan Abokanan sa Hausawa da suka saba da Juna, duk shekera ta kewayo sai su zo gidan sa idan basu same shi ba, to sai su tambayi matarsa suce "Ina Gana-Gana? Sai a ce ba ya nan ya tafi kasar Gara ganin ya'yansa.

Saboda yawan Na-nata sunan Gana- suna ce Gana-Gana fa? Shi ya haifar da sunan Gana-Gana wanda har yau ana kiran su da suna Gana-Gan kenan. Zuwan kabila, kafin wannan lokaci ana kiran-Gana-Gana da suna (ZHITAKO). Anan sunan Gana-Gana ya zama ganagana wadda har yanzu ana kiransu da shi watau Gana-Gana. Shi zane nan da ake gani a fuskar Gana-Gana, ko Nufawa ko Gara ai yayi asali ne. wata rana ne wani ya zamo daga sama sai icen kwara mai kaya-kaya ya fado masa a fuska sai yayi masa zane shi ke nan kowa kuma sai ya kama yin zanen shi ma yayi wa ya'yansa da ke kasar Gara shi ya sa duk inda kaga Nufawa ko Gana-Gana ko Gara duk zanen su daya ne sai dai wadansu Nufawa na su bai shi ga sosai ba. Su kuma Gara idan ka lura zaka gan zanan su ya zanen daya saboda su ya'yan Ganan da ke can kasar Gara wadda ubansu yazo yayi masu zane, suma haka suke zana fuskarsu su Gara sukan hada da salo har su na bille sanan zanen su. Shi kuwa Gana zaman sa a Gulu ya haifar da kasar Gana-Gana sabo da yaduwar iri. Watau Gulu da kewayen-sa abinda da ya kama daga katcha, Dangara, yaba, Ebo, Guridi, Kpada, Pelemi, Zago, da sauran garuruwa da suka kewaye duk asalin-su daya da Nufawa yadda ake cewa Gwarin gabas, Gwarin yamma, Gwarin Nkwa, da Gwarin Nge-Nge haka. Gana-Gana suke da Nufawa duk uwarsu daya ubansu daya Danjuma ne da Danjumai

## I:I KASAR GANA-GANA

Kasar Gana-Gana kasa ce mai yawan rayi-rayi da tuddai da tsakuwa da kuma ruwa, saboda ruwan rafin Gura-ra ya bi ta tsakiyar-su ne wani lokaci kuma sai a same shi ya baud'e ta bayan gari ko kuma yasa su a tsakiya. Shi wannan rayi-rayi suna nan kala biyu rayi-rayi mai laushi da mai danko. Saboda Noma da kuma Gini Domin suna da yawan son Noma da gini sosai sun fi Nomar doya, Rogo, shinkafa, da kuma rake. A wajen su, kuma ba'a bar su a baya ba saaboda ruwan da ya sa su a tsakiya. Manyan sana o'un-su sun had'a da rini, Noma, su, da kuma Gini duk inda ka gan Gana-Gana ba ka raba shi da

waddanan sana'a ko ina suka zauna zasu nemi inda za su cigaba da sana'ar su. Matarsu kuma kitso da sakan Gwado.

# CHAPTER:II

# AL'ADAR AUREN GANA-GANA

AL'adun auren gana-Gana, al'ada ce mai karfi mai wuya saboda mara-urata masu ci ma matar su mutun ci su yio hatara. Domin a kwai dokoki iri-iri da kuma kashe kudi wadda ko an hada mutun da kudi ya sake matarsa ko ya ci mata mutunci ba zai iya ba. Domin in ya duba wahaloli da ya sha to ba zai iya ci mata mutunci ba Al'ada ce wadda kafin ka auri yarinya za ka sha wuga sosai kuma bisa ga al'adun Gana-Gana idan ka aure ta ba saki tsakanin ta da kai zama ne za ku yi tankar wa da kabnuwa har mutu wa ta raba ku kuma ko mata hudu ne haka za ka kasance da su su kuma za ka gansu ka mar cyan uwar juna ba fada tsaakaninsu saboda haka a kyara zama aji Auren su da yadda ake Auren Gana-Gana, da ire-iren Auren su da yadda ake bukin auren su, da kuma ma'anar Aure.

## II:I MA'ANAR AURE

Aure alaka ce ta haliccin zaman tare tsakanin namiji da mace. Ana yin sa ne saboda abin da aka haifa ya sami asali, da mutunci, da kiwon iyaye. Kuma shi ne maganin zina da 'ya'ya marasa iyaye. Aure muhummin abune ga al'umma saboda haka akwai hanyoyi ayyananu da tabbatar da shi. Idan yaro ko yarinya suka guma sai iyayensu su sa ransu suyi. Masu Aure tun ransa bai yi halinsa ba. Wani lokaci kuwa yaro ne yake ganin yarinya ỳa rinka yi mata 'yar kyauta har a gane yana son ta sai a neman masa ita, ko abokansa su fada wa iyayen sa a gida cewa sun ga alamar wane yana son wance ko kuma a fada wa yarsa ko gwaggonsa, ko matar wansa, su kuma su I sar da sakon ga iyayensa.

## II:II IRE – IREN AUREN GANA-GANA

Auren Gana-Gana ya kasu kashi – kashi. A kwai Auren soyayya, Auren telas da Auren zumunta.

**AUREN SOYAYYA:-**

Auren ne wanda yaro ke ganin yarinya ya ce yana sonta da aure, ita kuma ta amince iyayenta sun yarda da maganar, sannan a yi haramar daurin aure.

**AUREN TILAS:-**

A nan yaro yakan gan yarinya ce, yace yana son ta da aure, amma ba ta amince ba. Iyayenta kuma su zartar da hukunci, watau wasu na so, ko suna ki. Har ma akan ba da yarinya ga wanda yake sa'ar mahaifinta ne ko sa'ar kakanta, alhali kuma ba ta so. Kuma akan nema wa yaro yarinya ba tare da yana so ba, saboda wata alaka ko yar jejeniya tsakanin iyayensu.

**AUREN ZUMUNTA:**

Wannan Aure ne wanda akan nema wa yaro yarinya daga cikin dagain uwa ko na uba, ba tare da an shawarci yaran ko yarinya ba. Irin wannan aure ana yin sa ne don kara yauka ka dan kon zumunci tsakanin 'yan uwa. Amma irin wannan auren akwai illa a ciki da zaran auren bai yi kyau ba to sai ka gan zuminci ya kusar rabuwa saboda rashin jituwar ma'a uran. Har ana wa wannan irin auren kirari da cewa "Auren Zumunta in ya yi kyau zumunta, in bai yi kyau ba mugunta". Allah ya gyara.

## II:III YADDA AKE YIN AUREN GANA-GANA

It al'adar gana-gana ta babbanta da sauran wasu al'adu domin ko za'a samu wadda suka zo daya to a cikin a l'uma to daya-daya za'a. samu al'ada wadda ta zo daya dana gana-gana sai a gyara zama a sha labari.

Yadda ake auren shi ne yarinya takan grma sosai ba irin grma nan na Hausawa ba da, irin ace yarinya shekara tara ko goma ko sha daya ba irin wannan girma. Zata yi ta tafi gidan miji ba. Gana-gana su kan bar yaran su mata su girma su cika har su batse har sai ta kusa tsufa agidan iyayan ta sannan wadda yake son ta sai ya zo ya yi magana da iyayenta sai a turo mutane daga gidan shi mijin su zo su yi magana. Idan yarinya ta yarda kuma iyayen. Sun amince, to sai ranar

kasuwa, ko wani buki idan ta tafi sai shi mijin watau saurayin mai niman tada aure ya 30 ya, kamata ya kai ta gidan sa. Idan tana son sa to sai zauna a gidansa har sai ta samu ciki ta haihu tukuna to wannan ya nuna akwai soyayya tsakanin ta da shi mijinta sai a dawo gidan su ayi bukin aure. Shi ango sai ya turo mutanen da su zauna a gidar amarya tare da iyayen ta har kwana goma sha.hudu kafin a kammala bikin auren har amarya ta dawo giden mijinta.

## II:IV YADDA AKE YIN BUKIN AUREN GANA-GANA

Bukin auren ya kama ne tun lokacin da ango ya aika da iyayensa gidan amarya. Iyayen ago za su yi kwana goma sha hudu ana hidmar buki sai asa masu kudin aure da abin da za su kawo. Arana ta Goma sha biyar za'a sa amarya alalle washe gari kuima shi ango zai kai manja garwa hudu da farin yadi alawayo da zanuwa da kayan abincin wadda za'a yi wa yan buki danguna da Abokan arziki. Kwana na goma shashida amarya za ta gudu kawaye za su boye ta har na inin guda sai ango ya biya wasu kud'a d'e tukun kafin amarya ta dawo sannan a kwana na goma sha bakwai sai a daura aure. Sannan sauran d angin ango. Su zo su tafi da amaryarsu gida. A nan amarya ba za ta ci abincin gidan ango ba har kwana bakwai za'a rinka kawo mata abincin daga gidan su kuma yawa cin abincin amarya shi ne shinkafa, da sakwara za'a yi su ne da manja idan an je kwasan tuwo to maimakan dan gwalan ruwa da ake yi to anan manja za'a dinga dangwala ana kwashen tuwon da shiko sakwara. Haka kuma ruwan wanka daga gidansu ne za'a kawo mata da sabulun solo da majigi da garin magani dakakke za'a hada shi gaba daya ayi ta wanka nakawana bakwai. A kwana na takwas za'a yi budan kai bayan buden kai amarya za ta zauna da kawayenta ana ta mutsuka mata lalle har matsayin kwana uku tukuna sannan amarya ta kafa murhu da yamma gabanin maga riba sai ta yi abinci ta kai wa angonta. Da safe kuma, sai ta dama kunu ta ba mijinta da sauran danguna da kawaye, da iyayen mijinta.

Ranar yin girkin, iyayen mijin, da na amarya zasu hadu a gindin murhu aga yadda amarya take girki. Idan ta iya shi ke nan sai a watse washe gari in kuma ba ta iya ba sai a ajiye mata tsohuwa wadda zata koyar mata da girki har sai ta iya. Idan kuma ta iya to sai akawo mata gara ayi mata danki kayan adon daki da kayan sawa sai ayi fatan Allah ya ba da zama lafiya. Wannan Auren da na zayyana muku a zama nin. Da watau Jahiliya amman yanzu daga yarinya ta cika ta isa zuwa aure sai a aura da ita ma wadda ta ke so sai miji ya kawo idukiya da sadaki da kayan dauran aure.

Sai iyaye su sa rana idan rana yazo sai a tara malla mai a raba goro na gayyatar mutane buki sai a daura aure akai amarya gidan mijin ta amman dudda haka sai ta kwana uku ana mutsuka mata lalle sanna ayi budan kai sai ayi mata dankin daki da kayan adon dakin da na sawa sanan kowa ya watse a b arta da angon ta sai kuma ayi fatan Allah ya bada ciki da goyo.

SERIAL/DOCUMENTATION UNIT
LIBRARY DEPT.
C.O.E. MINNA

## CHAPTER III:I

# HAI HUWA

Ma'anar Haihuwa ita ce yayin da miji da mata suka. Karu da samun da ko iya. Masomin haihuwa kuwa, shi ne, lokacin da mace ta sami juna biyu watau sa'ar da ta sami ciki bayan an tabbatar da igiyar aure tsakanin ta da mijinta. Karshen haihuwa kuwa shine yayin da jariri ya fito daga cikin uwarsa ta hanyar al'ada[1] Tun daga wannan lokacin ne iyaye za su shiga tattalin abin da suka samu har sai ya girma ya kai munzulin mutun watau ya isa kama kansa. To a cikin al'adun Gana-gana su, kan nasu al'adun ya babbanta da na Hausawa saboda su Hausawa sukan yi goyon ciki, goyon gida bayan 'yarsu ta haihu idan dan fari ne sai a ce ta tafi goyon gida to su Gana-gana ba su da wannan sai dai ta zauna a gidan mijinta har lokaci da ta haihu. To sai uwar mijinta, ko daya daga cikin danginta ta hannun uwarta ko kuma hannu uba ta zauna da ita ka fin ta haihu suna da wata al'adar da a ke kira Neman taimako.

## III:II NEMAN TAIMAKO

D.a zarar mace ta sami Juna biyu sai iyayenta ko wa su masu kula da ita su dukufa neman taimako don ta sauka lafiya. Wannan taimakon da zasu nema ba na kudi ko na abinci ba ne a'a wannan na neman lafiyar diyar su ne don dai ta sauka lafiyar Akan kafa mata dokokin da za ta kiyaye kamar kada ta rika cin abincin ko abin sha mai zaki, kamar zuma, ca suga da rake ko mazai kwaila ko alewa, sabo da saukin nauyin fitowar jariri ko jaririya wanda yakan faru da ciwon zaki. Akan kuma gargade ta ta kiyaye wasu tado di na mai ciki kamar rashin fita da dare, ko zuwa rafi da mangariba, ko rusunawa ta dade s aboda kiyaye ciwon baya. Su gana-gana suna da kula da mai ciki tun ciki na wata daya har ta haihu za'a kafa babban tu kunya a tsakiyar gida wadda yake cike da magani tana sha har ranar da za ta haihu. Ranar da aka ji ta sauka lafiya to wannan maganin sai a dauke shi daga inda yake. Wannan maganin da

ta sha zai taimaka mata har bayan rayurwarta a duniya domin ba wani maha luki w-anda da zai cuce ta hanyar magani ko cuta, duk wanda ya dauki mugun niyya da ita to sai ka gan mutun ya fadi ya mutu ba garan ba dalili kuma ba'a san cewa shi wannan muganta ne ya je yi, ya koma kan-sa ba. Haihuwa har wata kirari ake mata ana cewa "Haihuwa maganin mutuwa, ba don ke ba da iri ya kare kuma kyaun gida da magaji". To ta wannan hanyar da iyayen ke bi suna ceton ya'yan –su daga hannun makiya shi yasa ake tsoran Gana-gana har idan aka ce maka wannan Gana-gana ne sai ka ji an ce, "wai" "wai" ba ruwa na da mutanen kasar kudu. Ba ko me ba ne iyakarsa kenan kuma kai da ka sha wannan magani ba ruwan-ka da neman wata fitina ko yi niyyar yi wa wani to sai ka gan ya koma kan ka

## III:III GUDA

A kan yi guda sau uku idan namiji aka samu. Idan mace ce kuma guda buyu ne ake yi don nuna abinda aka samu. Watau shi guda tamkar. Shela ce, cewa ga irin abin da aka haifa sai kuma ita ungozoma, ta zo ta yanka cibiyar da ko yar da aka samu. Su Gana-gana suna da ungozoma ta musaman wadda ko da, da tsakiyar dare ne tayi sauri ta, tafi wurin da aka yi haihuwar ta sa ruwa a wuta na wanke da da kuma mai jego. Ita ungozoma ta kan yanke cibiyar da ko 'yo ta bune uwa watau mahifa saboda haka tunda ita ungozoma ta zo ta dauki abinda aka samu, to sai ta yi wa dan ko "yar wanka. Akan hàda sabulun salo da majigi da dusa a wanke dan fes kafin a samu sabulun zamani ayi anfani da shi sabo da fitar datti da maiko shi ya sa ake wanke abin da aka samu da sabulun salo da majigi da dusa saboda wadansu iya'yan su kan zo da kazanta to idan bai samu kyakyawar wanka ba to sai ka gan mutun ko ya glrma zai ta warin kashi. Ita wannan ungozoma takan samu matai makiya saboda lalura ko kuma tafiya ya ame ta. Shi kuma uban suna zaizo da matarsa da mutanen ta suyi rawa ana manna masu kudi tare da jariri ko jaririya da aka samu- Bayan

an gama a kwai kungiyarda aka nada watau kungiyar "yaran mata" da tsofaffi zasu hadu wuri guda a tattauna abubuwan daza'a yi da kuma kud'in da za'a tara wa maijego su wadannan kungiyar an zabe wata datijiya a ka ba ta "mamanyara" to ita waccan nan mammanyara ita ce zata kawo shawara da kuma kud'in da za'a tara. Su kuma wadannan yaran mata watau matasa (mata) za su kawo ruwa wajer durom hudu da kuma itace ko wacce cikin su zata tafi jeji ta kawo itacen hura wuta a kawo wa maijego da shi za" ayi anfani da shi, kuma maijego zata yi wankar jegon ta har ta fita Arba"in. da wannan itacen za'a yi abinci da shi ranar suna. Ita maijego zata dafa abinci tire biyu daya na mata, matasa daya kuma na kunguyar tsofoffi za'a cika tire sai su karba su rarraba wa kowa da kowa sai a tara wa maijego kudi' da sauran abinda za'a ba ta shi ke nan kowa sai ya watse ya koma gida sai dai a tara wa wata kuma wadda Alheri ya samu.

## III:IV WANKAN BIKI

Gana-gana dai ba su zuwa gida wankan buki. A gidan mijin suke zaunawa suyi wanka shi wannan wanka biki wanka ne na tilas da yarinya take yi ko ake yi mata da cewa ta sauka lafiya da tafasasshen ruwan zafin gaske. Hausawa su kan yi da runhu, ko sabara. Ko delbajiya saboda maganin sammatsin Ciwon sanyin haihuwa.

To Gana-gana ba su irin wanan wankar runhu ko delbajiya su suna anfani da kwarya ne sai a tsu-tsula wa mai jego, a nan tunda abin yazo yana kawo lahani ga wacce jinin ta ba karfi. Idan an tsula mata saita suma saboda haka, an hana wanka da kwarya sai da soshiya sai a dumbula ta a tafasassahen ruwan a zuba wa maijego. Haka za'a runka mata wanka safe da maraice, har kwana arbai'in idan ta gama wankar to sai a sauke tukunyar wankan sai ta shiga yi kwana daya-daya ama lura da ita har sai an tabbatar da ba cuta da ya shiga mata domin aka kuskure ba'ayi da kyau ba, ko ma ba'ayi shi ba sam-sam

duk cutar da ta sameta sai a dangata, ta da rashin wankar. A kwai kirarin da a ke wa wannan wankar.

"Wankar biki Maganin. Sumbwita, yarinya daure ki yi shi ki huta.

In kin kuskure shi sai buzunki[2]

## III:V KUNUN BIKI

Tun daga ranar haihuwa mai jegozata shiga shan wannan kunun za'a yi mata ne da kanwa ko a dan zuba mata, yaji ta sha shi dimi-dimi Gana-gana basu shan kumu kamar yadda Hausawa ke sha da sabara da kayan yaji ba. A'a shi yajin kadan kawai ake sa shi a kunu saboda maganin nan da ta sha shi tun tana da ciki to Gana-gana ba su ba da yaji ya yi yawa sai dai komai za ta ci, zata ci shi ne da zafi-zafi ba za'a barshi ya huce ba hakanan ruwan zafi idan ta ci abin ci bata da wata ruwan da zata sha sai na zafi saboda ciwon da ke ciki ya warke wai domin inda d'a ya fito ya warke. Sauran kayan barka da. Kayan kauri, da walima Gana-gana ba su yin shi.

SERIAL/DOCUMENTATION UNIT
LIBRARY DEPT.
C.O.E. MINNA

# CHAPTER IV:I

## ZANEN SUNA

Taron da ake yi bayan kwana bakwai da hai huwa domin a rada wa jariri ko jaririya sunan da aka zaba wadda za'a rinka kiranshi ko ita da shi, shi ake kiran zamen suna. To ana gobe suna akwai matar da ta ke raba suwit, da cingal gida-gida saboda sanar da jama'a cewa a kwai suna gobe-gobe. To ranar suna sai ungo zuma ta zo ta fito da jinjir, ko jinjira. Saboda a yi wa abin da aka samu wanka. Bayan anyi wa da ko 'yar wanka sai a. samu kaya mai kyau a sa mata ayi mata ko mishi ado saboda jama'ar da za su zo wurin suna da kuma kar ban jariri ko jaririya. Bayan rada suna akwai wasanni da ake yi na musamman don taya uban suna ko maijego murnar haihuwa. Wannan wasan, akan yi shi ne har ini guda. Za'a yi ta shagali ana kashe kudi.

## IV:II YADDA GANA-GANA KE WASAR SUNA

Bayan wanzami ya aske wa jariri ko jaririya kai sai mallamai su zo bayan rada. Suna da safe sai a ba wa jariri ko jaririya suna mai shala shi ma sai yayi shalar. Sunar da aka rada ya ce Allah ya raya wane kowance sai ayi adu'a a watse. To bayan watsewar mazan da suka zo rada suna nan fa za'a fara shagali. Maroki ko marokiya sai su zo da makadan su sai a fara wasa a gidan suna ana rera waka ana wasa uban jariri ko jaririya hannun uwa da na uba watau mutanen mai jego da mutanan uban da keya sai su zo suna manne – mannen kudi haka za'a yi tayi har rana ta kare. Acikin wannan wasa shi ne za'a kawo jaririya ko jariri a rike shi/ita ana wasa, ana wasa ta ana mata kirari ana manna mata kudi Gana-gana na da sunaye na gargajiya wadan da ake kiran mutane da su kama haka.

| Ranaku | Sunayen Gargajiya |
|---|---|
| Li Tani | Tani |
| Talata | Talatu |
| Laraba | Wusa ko Laba ko Gana (namiji) |
| Alhamis | Lami ko kashi |
| Juma'a | Ajuma |
| Asabat | Ashibi |
| Lahadi | Lade. |

Sunayen maza sun hada da kamar haka

| | |
|---|---|
| Abubakar | Abakare |
| Adamu | Adama |
| Muhammadu | Nmadu |
| Hassan ko Hassana | Abagi |
| Hussaini/Hussaina | Abako |
| Dan da yazo da kafa | Abini |
| Dan da aka haifa | |
| Da Cibiya a nade | Gunu |
| Awuyar sa. | |

## CHAPTER V.

# MUTUWA

Mutuwa kowa yasan rashi ne wadda akayi idan mutun ya rasu ya koma ga ubangijin sa an san ranar an yi rashinsa kenan sai dai ayi fatar Allah ya kara hakuri da dangana. Sai a aika wa mutane cewa anyi rashin wanccen ko wani sai kuma ayi zaman makoki da karbar ta'aziyar mutane kuma sai suzo su ta kawo sadaka da dafe-dafen abinci ma mutane da ke zuwa ta'a ziya har kwana bakwai sai mutane su taru da mallamai a yi adu'a wa Mammaci wadda ya mutu da fatan Allah ya jikan sa. Idan mace ce to sai mijin ta ya dan hakuri da danga-nanta da ya'yan ta da iyanyen ta. Idan kuma namiji ne matar sa sai ta yi zaman takaba har tsawan wata hudu ko biyar idan ta fita takaba sai a raba gado wa magada in kuma tana son zama ne gidan to sai ta cigaba da zama in kuma bata so to sai ta fita ta nemi wani miji wadda zata aura Ga al''adar Gana-gana kafin mutane su watse akwai dodonni da ake yi ana wasan mutuwa akwai dodonni maza wadda Gana-gana suke kiran sa (ANYI GABO). Watau maza ne zalla zasu yi wasan ayi ta rawa ana kida da dare ranar da aka yi bakwai wadannan dodonni ga su yi ta rawa har ini guda. A ini na biuu mata. Kuma sai su karbi fillisuyi tasa wasan. Shi kuma sunan wannan wasan shi ne (ALA MWA). Wannan Wasa na mata ne zalla zasu taru su yi ta kidi ana rawa ana buga ganga har na tsawon ini guda su ma. To bayan wanan wasan na mata, shi ke nan kowa sai ya watse magana yakare sai dai ayi tawa mamacin adu'a- Allah ya jikansa ya hada rai da gafara. Ko wa sai ya tara yanasa-yanasa ya koma gidan sa.

# CHAPTER VI

# BUKU KUWA DA WASANNI

Bukukuwa sun kasu kashi da yawa idan aka ce buki ana nufin taruwar farin ciki. Muna da bukin suna, da bukin sallah da bukin Aure. Dak lokacin da wadanan bukukuwa suka tashi akan yi wasanni sosai.

Jama'a su kan taru da yawa a yi ta wasanni iri-iri na farin ciki ana murna. Ga yadda ake yin sa daya kan daya.

6:1 **BUKIN SUNA**: Suna kowa dai ya san farin ciki ne wadda ta samu saboda Samun karuwa da aka yi. A na bukin suna ranar da aka rada wa yaro/yarinya suna. Sai a taru akiro maka da/mawaka a yi ta rawa ana manne-mannen kudi wadansu ma sukan kiro maijegon tazo ta yi rawa shagali ne akeyi har na ini guda sannan kowa ya watse.

## 6:2 WASAN SALLAH:

Wannan wasan akan yi sa ne ranan bukin sallah bayan an dawo daga masallacin idi. Babba da yara maza da mata duk sai a taru a fillin daddalin gari a yi ta rawa ana kida ana wasanni kala-kala wadansu sukan kai kamar kwana ki uki ko hadu kafin wasan ya kare.

6:3 **BUKIN AURE:** Wasa ne da ake yin shi domin nuna farin ciki. Akan taru ne maza da mata babba da yaro mawaka da makada zasu taru ayi ta rawa ana manna kudi gidan ango da na amarya zasu taru ayi ta famar wasa da Naira ana manna wa A marya da ango kudo da kuma abokannan arziki har na koma guda kafin kowa ya watse.

## WASAN SABON DOYA

**6:4.**

Shi wannan wasan ana yai sa ne ranar da sabon doya ya fito, to ba wadda zai kai doya bakin sa kuma ba bu wanda zai sayar da doya sai an yanka shi kanana in za'a bare bawon sanan a zuba masa manja akai hanya a ajiye za'a samu katanga fasashe a zuba a ciki. Sannan a kai hanya a ajiye shi a dawo a ci gaba da wa sanne. Do donne zasu taru ana buga ganga ana rawa ana

# CHAPTER VI
## BUKU KUWA DA WASANNI

Bukukuwa sun kasu kashi da yawa idan aka ce buki ana nufin taruwar farin ciki. Muna da bukin suna, da bukin sallah da bukin Aure. Dak lokacin da wadanan bukukuwa suka tashi akan yi wasanni sosai.

Jama'a su kan taru da yawa a yi ta wasanni iri-iri na farin ciki ana murna. Ga yadda ake yin sa daya kan daya.

6:1 **BUKIN SUNA**: Suna kowa dai ya san farin ciki ne wadda ta samu saboda Samun karuwa da aka yi. A na bukin suna ranar da aka rada wa yaro/yarinya suna. Sai a taru akiro maka da/mawaka a yi ta rawa ana manne-mannen kudi wadansu ma sukan kiro maijegon tazo ta yi rawa shagali ne akeyi har na ini guda sannan kowa ya watse.

### 6:2 WASAN SALLAH:

Wannan wasan akan yi sa ne ranan bukin sallah bayan an dawo daga masallacin idi. Babba da yara maza da mata duk sai a taru a fillin daddalin gari a yi ta rawa ana kida ana wasanni kala-kala wadansu sukan kai kamar kwana ki uki ko hadu kafin wasan ya kare.

6:3 **BUKIN AURE:** Wasa ne da ake yin shi domin nuna farin ciki. Akan taru ne maza da mata babba da yaro mawaka da makada zasu taru ayi ta rawa ana manna kudi gidan ango da na amarya zasu taru ayi ta famar wasa da Naira ana manna wa A marya da ango kudo da kuma abokannan arziki har na koma guda kafin kowa ya watse.

### WASAN SABON DOYA

6:4.

Shi wannan wasan ana yai sa ne ranar da sabon doya ya fito, to ba wadda zai kai doya bakin sa kuma ba bu wanda zai sayar da doya sai an yanka shi kanana in za'a bare bawon sanan a zuba masa manja akai hanya a ajiye za'a samu katanga fasashe a zuba a ciki. Sannan a kai hanya a ajiye shi a dawo a ci gaba da wa sanne. Do donne zasu taru ana buga ganga ana rawa ana

waka har na kwanaki bakwai. Wannan wasan maza zalla ke yin sa kawai bayan kwana bakwai sai a fara cin sabon doya.

## CHAPTER VII

## DANGANTAKAR AL'ADUN GANA-GANA DA NA HAUSA WA

Dangantaka tsakani Gana-gana da Hausawa bashi da yawa domin basu da wata dangantaka mai tsanani hakanan sa boda su karan kan su basu ji Hausa ba suna kiran Namiji "Ke" mace kuma "Ka" ke nan kun san cewa dangantakar zai yi wuya sai dai wajen kiran sunayen wadansu abubuwa ya kan shi ga juna da na Hausawa. Sunaye kamar haka

| Gana-Gana | Hausawa |
|---|---|
| Buta | Buta |
| Kofi | Kofi |
| Fitilla | Kitilla |
| Talatu | Talatu |
| Tani | Tani |
| Asabe | Asabe |
| Ladi | Ladi |

To dangantakar Hausawa da Gana-gana kuma shi ne tun da Gana-Gana da Nufawa daya ne, akwai dangantaka tsakamin su da katsinawa har suna karban kudin sha'ara da juna kuma suna wasa da junanasu. Duk inda aka hadu zaka ji cacan baki na tashi tsakanin-su. Katsinawa su ce sune babba. Nufawa suce sune. Haka ma Gana-gana domin an dauke su duk daya ne 'yan uwar juma ne.

## KAMMALAWA

Duka-duka na kammala aiki na tun daga farko mun yi magana kan tarihin Gana-Gana, da al'adunsu. Ma'anar aure kamar yadda muka ce Aure dangataka ce tsakamin namiji da mace don hallicin zama tare. Haka kuma mun ga yadda Al'adan auren Gana-Gana ta ke da kuma ire-iren aurensu. Kamar. Auren soyayya, Auren tilas, da kuma na zumunta. Haka kuma mun gan yadda kasar gana-gana take da Yadda zanen su ya sami asali mun kuma gan yadda da ake bukin suna watau haihuwa da kuma bukin mutuwa da wa sanni iri-iri.

Daga nan kuma mun ga Dangantakar ala'adar Ganagana da na Hausawa da kuma karin bayani a kan sunan gargajiya wadda suke kinran mutanen su da shi. Sunanyen Ranaku, da kuma sunayen da ake kiran mata da su da kuma sunayen maza. A karshe dai Godiya ya tabbata ga Allah madaukakin Sarki Alhamdulillahi.

Wadda ta rubuta

**Hajiya Hajara Halidu Dangara.**

LITA FIN DA NA DUBA
DA

| | |
|---|---|
| WADDA TA BANI TARIHI | LITAFIN<br>ZAMAN HAUSAWA BUGU<br>NABIYU NA<br><br>HABIB ALHASSAN USMAN<br>IBRAHIM RABIU<br>MOHAMMED ZARRUK. |
| WADDA TA BADA TARIHI | - NANA AISHATU<br>ABUBAKAR JIWO<br>DANGARA<br>(MAHAIFIYATA) |

**Hajiya Hajara Halidu Dangara.**

LITA FIN DA NA DUBA DA

| | |
|---|---|
| WADDA TA BANI TARIHI | LITAFIN ZAMAN HAUSAWA BUGU NABIYU NA<br><br>HABIB ALHASSAN USMAN<br>IBRAHIM RABIU<br>MOHAMMED ZARRUK. |
| WADDA TA BADA TARIHI | - NANA AISHATU ABUBAKAR JIWO DANGARA (MAHAIFIYATA) |